## Addu'ar mika kai ga bin Yesu Kristi

*Na gaskanta da Allah daya, Mahalicci, Uba Mai iko duka:*

*Ina kin dukan alloli*

*Na yarda cewa nayi zunubi gaban Allah, na kuma yiwa mutane zunubi.  Ta wurin yin haka, na yiwa Allah rashin biyayya, na kuma yi masa tawaye, na ketare dokokinsa*

*Ba zan iya kubutas da kaina daga zunubi ba.*

*Na Gaskanta Yesu shine Almasihu, Dan Allah wanda ya tashi daga matatu.  Ya mutu a bisan giciye a madadi na, ya kuma dauka wa kansa hukumci domin zunubaina.  An tashe shi daga matattu domina.*

*Ina juyawa ga barin zunubaina*

*Ina rokon kyautar gafarar nan da Kristi ya samo nasararta a bisan giciye.*

*Na karbi wannan kyauta ta gafarar a yau*

*Na zabi in karbi Allah a matsayin Uba na, na kuma yarda in zama nasa.*

*Ina neman kyauta ta rai na har'abda.*

*Ina mikawa Kristi mulkin rayuwata, ina kuma gayyatarsa da ya zama Ubangijin rayuwata daga wannan rana zuwa nan gaba.*

*Na tsinke kowace irin dangantaka ta ruhaniya wadda ba ta Kristi ba ce.  Ina raba kaina da Kalmar Shahada da dukan hakkin da take da ita a bisa na.*

*Ina kin Shaidan da dukan muguntarsa.  Na tsinke kowace yarjejeniya wadda na shiga da miyagun ruhohi da kuma dukan abin da yake da wata alaka da Shaidan.*

*Na rabu da dukan dangantaka ta mugunta da wadanda suka dora kansu a bisana.*

*Ina tsinke dukan munanan alkawalai wadanda suka shafi rayuwata da kakanni na suka shiga a madadina,*

*Ta wurin Yesu Kristi, ina kin kowace kwarewa ko iya yin duba wanda ba daga Allah yake ba.*

*Ina roko domin kyautar Ruhu Mai Tsarkin da aka yi alkawalinsa.*

*Allah Uba, idan ka yarda, ka yantar da ni, ka kuma canza ni domin in kawo daukaka a gareka, kai kadai.*

*Ka sani a cikin diyan Ruhu Mai Tsarki domin girmamaka in kuma kaunaci mutane.*

*Ina furta cewn  na kebe kaina na kuma kulla dangantaka da Allah ta wurin Yesu Kristi a gaban jama'a da kuma gaban dukan ikoki na ruhaniya.*

*Ina furta cewa ni magaji ne na Sama.  Allah shine kariyata.  Da taimakon Ruhu Mai Tsarki, ina zaba in mika kai, in kuma bi Yesu Kristi shi kadai a matsayin Ubangiji na dukan kwanakin raina.*